# LESSON 24

Baba ta dafa abinci. Dukkanin mutanen gida kowa ya ci abinci ya ƙoshi. Saboda abincin ya yi daɗi kuma an yi shi a wadace. Baba ne ya sayo kayan abincin sannan kuma ya bayar da kuɗin cefane.

Lokacin da zai tafi kasuwa tare suka tafi da ɗan'uwana. Da suka tashi dawowa shi ɗan'uwan nawa ne ya ɗauko kayan da suka saya.

To ka ga yanzu Baba da Baba da ɗa'uwana kowa ya bayar da tasa gudunmawar kai har ma da 'yar'uwata da ta yi wanke-wanke ita ma ta bayar da tata gudunmawa. Haka ake rayuwar iyali a ƙasar Hausa; kowa da irin gudunmawar da yake bayarwa daidai da shekarunsa.

Ina fata wannan halayya za ta zama kyakkyawar abar koyi ga sauran al'ummomi.